# FADAKARWA

## A kan: Sanin makamar kasuwanci

## <u>Kashi na 3a:</u> Mahimmancin adana bayanai

### Mene ne adana bayanai

- Adana bayanai wani tsari ne na rubuta duk wata hada-hadar ciniki a kasuwa ko kanti. Wannan ya hada da kayan da a ka sayar da kuma wadanda a ka sayo.
- A na adana wadannan bayanai ne daki-daki.
- A na kuma rubuta bayanan ne a kai a kai, ko kuma da zarar an yi ciniki ko an sayo kaya, ko da lokacin da kanti ke rufe ne.

### Muhimmancin adana bayanai

Adana bayanai yana bawa dan kasuwa damar:

- Sanin adadin kayan da a ka sayar ko yaushe.
- Sanin adadin kayan da suke a kanti ko a suto.
- Sanin kudin da suka shigo masa.
- Sanin kudin da suka fita daga hannunsa.
- Sanin yadda zai inganta harkokinsa domin samun karin riba.
- Sanin ko harka riba ko faduwa a gare shi.
- Bibiyar gudanar kasuwa yadda zai iya hango wata matsala kafin ta zo gare shi.
- Sanin kayan da su ka fi karbuwa da farin jini a kasuwa.
- Sanin kayan da ya kamata a sayo.
- Sanin abokan ciniki da yawan harkokin da a ke yi da kowannensu. Wannan zai sa dan kasuwa ya san kimar abokan cinikinsa.
- Sanin yawan cinikinsa da karfinsa a kasuwa. Wannan zai iya yin amfani wajen neman lamuni ko bashi.
- Tabbatar wa abokan ciniki cewar ya san abin da ya keyi. Wannan zai sa su ji dadin harka kuma su saki jiki da shi.
- Tsara harkokinsa sosai da kuma yanke hukuncin da ya dace ko da yaushe.
- Gane inda dan kasuwa yake da rauni domin ingantawa.